# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na tara: Hatsabibin yaro

Wanda ya rubuta: Nkoji C. Muhoho
Wanda ya tace: Maja Braun
Wanda ya fassara: Kabir Isa Jikamshi

**’Yan wasa:**

Sama’ila: ɗan shekara 17
Hadiza: ’yar shekara 15
Bilkisu: ’yar shekara 40
Mariya: ’yar shekara 43
Adamu: ɗan shekara 36
Dokta Husaina: ’yar shekara 34

**MAI GABATARWA:**

Masu saurarenmu, lale marhabin da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” game da kiwon lafiya mai taken yadda za a nisanci kamuwa da cutar gudawa. A wasan da ya gabata kun ji yadda Hadiza da Sama’ila suke nuna damuwa game da yanayin banɗakunan makarantarsu. Amma an tsaftace banɗakunan bayan da jami’in kula da lafiyar garin, Uncle Adamu, ya ba da shawara inda aka sa wa ramukan yin bayan-gida marafai, aka kuma fara wanke banɗakunan a kai-a kai tare da yayyafa toka a kan daɓen sumuntin wurin. Ɗaukan waɗannan matakan ya taimaka wajen dakatar da yaɗuwar ƙwayoyin cutar gudawa. Sai a biyo mu a yau domin jin yadda za ta ɗore a wannan shirin.

**Fitowa ta 1: A gidan Mariya**

Sama’ila, Hadiza

| | |
|---|---|
| **SAMA’ILA** | Hadiza… Hadiza… kina nan? Kina gida? Hadiza… Hadiza… Na san cewa kina wani wuri a nan. Hadiza, kina nan kuwa? |
| **HADIZA** | Shshhhh, ka daina! Ka daina ƙwara mini kira haka! Ka yi shiru mana! |
| **SAMA’ILA** | Saboda me ba za ki amsa kirana ba? |
| **HADIZA** | Shshhh, ka yi shiru mana! Ina nan, ina ɗakin Mama. Tsit! Za ka ta da yaro. |
| **SAMA’ILA** | Haba! Ban san cewa kina sake yin renon ɗan maƙwabtanku ba ne. |
| **HADIZA** | Ka manta cewa, yau ne mamanshi take zuwa kasuwa, don haka nake zama da yaron a duk tsawon rana**.** |
| **SAMA’ILA** | Ki yi haƙuri, na manta. Shekarun wannan yaron nawa, kika ce? |

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Da farko, sunanshi Kabiru. Shekarunshi takwas. Bari mu fice daga nan kafin ka ta da shi. Na sha fama kafin ya yi barci, kuma kunnuwansa kamar na zomaye suke! |
| **SAMA'ILA** | Zomo? |
| **HADIZA** | Yana yin barci sama-sama. Yana farkawa a kai-a kai, ya riƙa susar jikinsa. Duba, yana da wasu alamomi a kan fatar jikinsa. |
| **SAMA'ILA** | Mene ne ya same shi? Yana kama da… da ɗan shekaru uku zuwa huɗu. |
| **HADIZA** | Haka ne, ga alama dukan 'yan gidansu suna da ƙaramin jiki. Ka tuna 'yar'uwarsa Jamila? Shekarunmu ɗaya da ita, amma a yanzu haka, na yi biyunta a girma. |
| **SAMA'ILA** | Kina nufin wannan kyakkyawar budurwar marar jiki, mai fara'a sosai? |
| **HADIZA** | Ba kyakkyawa ba ce. Ba ta da ƙiba ne kawai, tana kama da 'sikla'. Takan yi fashin zuwa aji a kai-a kai. |
| **SAMA'ILA** | To, shi ke nan! Na ji ba kyakkyawa ba ce. Amma saboda me take fashin zuwa aji? |
| **HADIZA** | Ka tuna lokacin da ka yi fama da cutar gudawa, wadda ta sa ka kasa zuwa makaranta tsawon makwanni biyu? A gaskiya, kusan ko da yaushe Jamila tana fama da gudawa, don haka takan yi fashin zuwa makaranta. |
| **SAMA'ILA** | Amma don me ba ta samu magani ba? |
| **HADIZA** | Sama'ila, ni 'yar ajinsu ce kawai, ba mahaifiyarta ba ce! |
| **SAMA'ILA** | To shi ke nan. In haka ne, ina dai mamaki… ina nufin ina tausaya mata. |
| **HADIZA** | Don me ka damu da ita ne? Ba ka ma san ta ba. Ba makwabciyarku ba ce. |

**SAMA'ILA** Yi haƙuri, Hadiza, yi haƙuri! Ke ƙawata ce, kuma ba kya fama da wata rashin lafiya kamar ita.

**HADIZA** Shi ke nan, amma ya kamata ka san cewa ita daƙiƙiya ce. Tana da sanyin jiki, kuma ita….

**SAMA'ILA** Ki daina cin fuskar 'yar ajinku!

**HADIZA** Sama'ila, ina faɗa maka, ko a lokacin da ba ta fashin zuwa aji, ita take yin na ƙarshe a jarrabawa.

**SAMA'ILA** Hadiza, kina dai kishi ne kawai!

**HADIZA** Yanzu, dubi! Dubi abin da ka yi, Sama'ila.

**MAI BA DA LABARI:**
Tirƙashi! Duk da yake Hadiza da Sama'ila ba wasu ƙwararru ba ne, amma kuma suna iya gane yaran da suke da ƙanƙantar jiki idan aka yi la'akari da shekarunsu, ko kuma ake barinsu a baya wajen fahimtar darasi a cikin aji. Bari mu ci gaba da saurare domin mu ji dalilan da suka sa Jamila take daƙiƙanci a cikin aji, shi kuma Kabiru yake da ƙaramin jiki duk da yake shekarunsa takwas.

**Fitowa ta 2: A gidan Bilkisu**
Bilkisu, Adamu, Dokta Husaina, Hadiza, Sama'ila, Mariya

**BILKISU** Adamu da Dokta Husaina, ko kun san irin farin cikin da nake yi dangane da yadda kuke kawo mana ziyara a kai-a kai? Kai ɗan'uwa ne na gari. Ita ma Husaina, duk da tarin aikin da take yi a asibiti, takan ware lokaci ta zo ganinmu! Da mijina, watau ɗan'uwanka, zai iya ganinmu daga wurin da yake yanzu, da ya yi murna sosai! Allah ya ji ƙanshi.

| | |
|---|---|
| **ADAMU** | Amin, Bilkisu! Wannan yana ɗaya daga cikin ayyukanmu, mu riƙa kula da ke da kuma Sama'ila, musamman ma bayan abin da ya faru da jinjira Fati. |
| **BILKISU** | Ita ma Allah ya sa ta huta. Amma yanzu kam hankali ya kwanta game da sakamakon waɗannan gwaje-gwajen da aka yi mana. Babu sauran cutar gudawa a cikin gidana, haka ma a gidan Mariya da 'yarta Hadiza. Kun san cewa, na ɗan yi fargaba lokacin da aka gwada mu. |
| **ADAMU** | Na sani mana. |
| **DR HUSAINA** | Yana yanayin lafiyar Sama'ila? Ina yake? |
| **SAMA'ILA** | Kawu Adamu, Anti Husaina, lale marhabin! |
| **HADIZA** | Uncle Adamu, Anti Husaina, sannunku da zuwa! |
| **ADAMU** | Sannunku! Yaya kuke Sama'ila, kai da Hadiza? Yanzu-yanzun nan muke maganarku. |
| **DR HUSAINA** | Hadiza, kin zo mana da wani baƙo? Wane ne wannan yaron? |
| **HADIZA** | Kabiru ne, ɗan makwabciyarmu. Ina cikin renonsa, sai Sama'ila ya shigo ya ta da shi daga barci. Daga nan kuma sai na ji rurin motarku. |
| **ADAMU** | Yana da kyau ƙwarai, ki riƙa yin reno. |
| **SAMA'ILA** | Hadiza tana renon wani yaro ɗan matsitsi. |
| **BILKISU** | Sama'ila, zo! Wannan bai dace ba. |
| **HADIZA** | Sama'ila, ba laifinsa ba ne, ga alama dai zai ci gaba da kasancewa maras girman jiki ya zuwa wani lokaci mai tsawo. Ga alama, bai taɓa nuna alamun zai yi girma sosai ba. |
| **BILKISU** | Kuma a duk lokacin da na ga wannan yaron yana susan jikinsa, sai ka ce wanda yake da ƙuma a dukan jikinsa. |
| **DR HUSAINA** | Yaro abin tausayi! Kabiru… Kabiru, ɗana, zo nan! Zo nan in duba ka. Kuma ya yi shiru, sai ka ce bai iya magana ba. |

**SAMA'ILA** Dokta Husaina, ya kuma kamata mu kira 'yar'uwarsa kyakkyawar nan, wato Jamila, domin ita ma ki duba ta. Tana da rama sosai, kuma kusan ko da yaushe tana rashin lafiya.

**HADIZA** Ba kyakkyawa ba ce! Tana fama da cutar gudawa, kuma tana da sanyin jiki, kanta ba ya ja.

**BILKISU** Kal! Ku daina abin da kuke yi.

**DR HUSAINA** Adamu, ka duba wannan kuwa? Shin ka lura da waɗannan alamomi a kan fatar jikinsa? Shakka babu, kuma nauyinsa ya kasa, idan aka kwatanta da shekarunsa.

**ADAMU** Muna da wata babbar matsala. Jikin Kabiru ya tsunbure.

**BILKISU** Adamu, ka iya bakinka game da abin da kake faɗa kan 'ya'yan makwabtanmu. Za ka iya jefa mu a cikin wani gagari!

**DR HUSAINA** Ban damu da abin da makwabta za su faɗa ba, amma abin da nake faɗa miki shi ne, wannan yaron yana buƙatar taimakon asibiti cikin hanzari.

**HADIZA** Haba! Anti Husaina, za ki iya taimaka mishi ya yi tsawo?

**DR HUSAINA** Hadiza, girman Kabiru ya yi ƙanƙanta ƙwarai a yaron da ya kai shekarunsa na haihuwa. Yana da abin da muke kira, tsunburewar girma.

**HADIZA** Mene ne ya sa ya ƙanƙance?

**BILKISU** Hadiza, na tabbata Dokta Husaina za ta shawarci maman Kabiru game da yadda zai samu lafiya. Yanzu haka ma, ina jin mamansa ta dawo gida. Ki mai da shi wurinta, sannan ki shaida mata cewa, Dokta Husaina za ta zo ta gan ta ba da daɗewa ba.

**SAMA'ILA** To, mene ne yake damunsa?

**DR HUSAINA** Sama'ila, ka tuna tsutsar cikin da ka samu lokacin da ka yi fama da cutar gudawa? Kabiru yana da tsutsotsin ciki, amma

| | |
|---|---|
| | wasu ne na dabam. Mai yiwuwa yana da fararen tsutsotsi a cikin cikinsa. |
| **BILKISU** | Tsutsotsi! Ta yaya yaron ya same su? |
| **ADAMU** | Bilkisu, kin tuna abin da muka koya tun daga farko-farko game da dalilin da ya sa muke wanke hannuwanmu, da tafasa ruwa, sannan kuma muke tsaftace abincinmu? A taƙaice, waɗannan tsutsotsi suna zama a cikin 'yan hanji. Kuma domin su girma, dole su riƙa samun abincinsu daga wurin yaron. |
| **SAMA'ILA** | Haba, a'a, wannan mugunta ce! |
| **BILKISU** | Ɗan yaro da shi, abin tausayi. |
| **DR HUSAINA** | To, bari dai mu jingine wannan magana. Tsutsotsin suna raba abinci da Kabiru, wanda shi ne ya kamata ya taimaka masa ya yi girma. Kazalika, fararen tsutsotsin suna kuma samun abincin da zai gina jikinsu ta hanyar shan jini daga jikin yaro. Kowace tsutsa sai ta riƙa shan jini ɗan kaɗan. Kuma yaron da ya kamu, zai iya samun ɗaruruwan irin waɗannan tsutsotsi a cikin cikinsa. Idan kuma aka ci gaba da yin biris da matsalar, tsutsotsin za su ci gaba da ƙaruwa, sannan ƙarin illolinsu, su ci gaba da bayyana. |
| **SAMA'ILA** | A'a, haba! Wannan baƙar mugunta ce kawai. Ga shi kuma mutane ba su san yadda za su yi rigakafinta ba. Kuma abu ne mai sauƙi. Ya zama wajibi mu yi wani abu game da ita. |
| **ADAMU** | Ai ba nan matsalar ta tsaya ba kawai. Yaron zai iya fama da gudawa sosai, haɗe da mashasshara. |
| **BILKISU** | Lalle, Adamu, wannan cuta fa ga alama tana da muni sosai. To mene ne kuma ya samu fatar jikinsa? Na san ka ga duk waɗannan tabubbuna da kirci-kirci da ke jikinsa. |
| **DR HUSAINA** | Kin ga, 'yan tayin fararen tsutsotsin… |
| **SAMA'ILA** | 'Yan tayi? Mene ne wannan? |

**ADAMU** Ka yi tambaya mai kyau, Sama'ila. Su ne zan iya cewa tsutsar da ba a kammala halittarta ba.

**DR HUSAINA** Idan mutum ya harbu da irin wannan tsutsa, wadda ake samu a wurare marasa tsafta dabam-dabam, za ta shiga cikin fatar jiki. Idan ta yi haka, daga nan sai wurin ya fara yin ƙaiƙayi, sai wasu 'yan alamomi su fara fitowa. Daga nan kuma sai wannan ɗan tayin tsutsa ya yi ƙaura ya koma cikin hanyoyin jini. Za ta kuma iya kaiwa ga huhu ta kafar hanyoyin da suke kai wa huhun iska.

**SAMA'ILA** Ina jin na fahimci cewar wannan tsutsa takan tafi rangadi a cikin jikin mutum.

**ADAMU** Abin gwanin ban sha'awa yadda ka fahimta. Amma wani rangadi ne fa mai illa.

**BILKISU** Husaina, don Allah ki ci gaba, hankalina yana karkatowa ga abin da nake ji.

**DR HUSAINA** Daga nan 'yan tayin tsutsar za su shiga cikin ƙananan 'yan hanji, inda daga ƙarshe kuma su gawurta, su zama balagaggun tsutsotsi.

**SAMA'ILA** Dokta Husaina, don Allah mu tafi yanzu. Mu je mu ɗauki Kabiru mu kai shi asibiti. Kuma a gaskiya, ya zama wajibi mu samo hanyoyin da za mu ilimantar da sauran jama'ar gari game da wannan matsala.

**MARIYA** Wa ya gane mini wannan malallaciyar 'yar tawa?

**ADAMU** Ina kwana, Mariya? Mene ne haka na ga kin yi sammako, ko ma kin ce "kun tashi lafiya"?

**MARIYA** Aaah… Ina kwananku? Kun tashi lafiya? Shin ko Hadiza tana nan?

**BILKISU** Tana can wurin Maman Kabiru. Mu ma muna daf da tafiya can.

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Saboda me? Maman Kabiru ta zama wurin yawon buɗe idanu ne? Mu dai mun san cewa, ita maman wani guntun yaro ne da wata daƙiƙiyar yarinya. |
| **DR HUSAINA** | Kabiru yana da tsutsotsin ciki, da ita kuma… mene ne sunanta ma? |
| **MARIYA** | Sakaryar daƙiƙiyar yarinyar? Sunanta Jamila. |
| **DR HUSAINA** | Ta san abin da take yi. Ba ta dai da lafiya ne kawai. |
| **MARIYA** | Babu shakka, haka take, amma dai daƙiƙiya ce. |
| **BILKISU** | Mariya! Wani lokaci ke muguwa ce! |
| **ADAMU** | Don Allah, ko za mu saurara? Wannan yana da matuƙar muhimmanci. |
| **DR HUSAINA** | Watakila Jamila ta daɗe da irin waɗannan tsutsotsin ciki a jikinta. Idan aka haɗa matsalar cutar gudawa da takan yi fama da ita, ga shi kuma tsutsotsin suna samun abinci daga jikinta, hakan yana nufin za ta kasance maras saurin girma, kuma ba za ta yi saurin koyon abu ba. |
| **ADAMU** | Ina dai fata, ba mu yi jinkiri sosai ba wajen tunkarar matsalar. |
| **MARIYA** | Mu… mu? Adamu, sai ka faɗa mini yadda na shiga cikin wannan? Ba laifina ba ne. Yanzu abin da zan yi shi ne, in garzaya zuwa can domin in kuɓutar da yarinyata mai basira kafin ita ma ta kamu da cutar tauyewar ƙwaƙwalwa. Na tafi. |
| **BILKISU** | Mariya! Ke dai muguwa ce! |
| **DR HUSAINA** | Dukanmu za mu tafi wurin Maman Kabiru. Dole ne ’ya’yanta su tafi asibiti nan take. |

**MAI GABATARWA:**

Da fatan masu sauraro za su riƙa yin hasashen abin da zai wakana nan gaba. Sai a dakace mu a shiri na gaba domin jin yadda za a ƙarke. Kafin nan ana iya ziyartar adireshimu na yanar gizo, wato www.dw.world.de/lbe, domin sake sauraron wannan shirin da ma wasu.